# Duk mutumin da ya halarci (yaƙin) Badar da Hudaibiyya ba zai shiga wuta ba

Daga Jabir - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Duk mutumin da ya halarci (yaƙin) Badar da Hudaibiyya ba zai shiga wuta ba".

[Ingantacce ne] [Ahmad ne ya ruwaito shi kuma asalinsa yana cikin Sahih Muslim]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa duk wanda ya halarci yaƙin Badar wanda aka yi a cikin shekara ta biyu da hijira yana mai yaƙi tare da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, haka nan wanda ya halarci Sulhun Hudaibiyya, kuma a cikinsa ne aka yi Bai'atir Ridwan wacce aka yi a cikin shekara ta shida da hijira ba zai shiga wuta ba.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee